# Masu Rubuto Buƙatar Samun Kariya a Matakin Ƙasa-Da-Ƙasa

**Ɓangaren Taƙaitawa**

A Bank of Ireland, abin alfahari ne a gare mu yadda muke bunƙasawa da inganta al'amuran hada-hadar kuɗin kwastomominmu. Ƙashin bayan bunƙasa hada-hadar kuɗi shi ne ya kasance ana yi da mutum a ɓangaren hada-hadar wanda hakan ke tabbata yayin da al'umma ke da damar cin gajiyar dukkannin ayyukan da banki ke gudanarwa. Muna tallafa wa masu rubuto buƙata na samun kariya a matakin ƙasa-da-ƙasa ta hanyar samar musu damar cin gajiyar ayyukan da banki ke gudanarwa tare da samar da tsarin tafintanci domin tabbatar da cewa sun samu taimakon da suke buƙata dangane da harƙallar kuɗaɗensu.

Muna da tsare-tsare nau'uka biyu da suka shafi harkar gudanar da banki na yau da kullum, waɗanda za su dace da masu rubuto buƙatar samun kariya na matakin ƙasa-da-ƙasa. Akwai keɓantaccen akawun na current da kuma akawun ɗin banki gama-gari. Dukkanninsu biyu za su samar maka da wuri mai aminci na adana kuɗinka wanda za ka iya kaiwa gare su a kowane lokaci. An samar da cikakken bayani game da waɗannan akawun-akawun tare da jerin takardu da ake buƙata domin buɗe waɗannan akawun-akawun.

Da zarar ka tanadi dukkannin takardun da ake buƙata, to za ka iya zuwa ɗaya daga cikin ressan Bank of Ireland wanda daga nan za mu bi matakan buɗe maka akawun.

Mun san da cewa wataƙila waɗansu kwastomomi ba su iya harshen Inglishi ba ko kuma suna ji amma kaɗan, wanda ba za su iya magana da Ingilishin ba yayin da suka je banki. Idan ta kasance haka gare ka, to za ka iya zuwa da aboki, abokin aiki ko tafinta wanda zai riƙa maka tafintanci.

Bugu da ƙari, ma'aikatan Bank of Ireland da dama sun iya harsuna daban-daban sannan za mu yi bakin ƙoƙarinmu wajen taimaka maka idan ba ka da wanda zai iya maka tafintanci. Kawai ka tambayi Mai Ba Ka Shawara a nan reshen bankin.

Za ka iya samun cikakken bayani game da ressan bankinmu a nan https://www.bankofireland.com/branch-locator/

Classified as Public (Green)